# Ya ku mutanen Madina, Ban sameku Batattu ba sai kuma Allah ya shiryar da ku da ni?kuma kun kasance kan ku a rarrabe sai kuma ya hada kanku dani ? kuma kuna talakawa sai Allah ya Azutaku sabida ni?

Daga Abdullahi Dan aid Dan Asim ya ce: yayin da Allah ya kwaranyo Arziki ga Manzonsa a ranar yakin Hunain; sai ya rabawa Mutane, haka ga wadanda ake janyo hankalinsu zuwa Musulunci, kuma bai bawa Mutanen Madina komai ba, kamar wani abu ya dan sosa musu rai; don bai basu komai ba kamar yadda ya bawa Mutane, sai yayi Huduba yana mai cewa: Ya ku mutanen Madina, Ban sameku Batattu ba sai kuma Allah ya shiryar da ku da ni? kuma kun kasance kan ku a rarrabe sai kuma ya hada kanku dani ? kuma kuna talakawa sai Allah ya Azutaku sabida ni? ko yaushe yace wani abu sai su ce Allah da Manzonsa sune mafi baiwa a gare mu, sai ya ce Mai ya hanaku ku Amsawa Manzon Allah? sai suka ce: Allah da Manzonsa sune mafi baiwa a gare mu, sai ya ce: da kun so da kunce ka zo mana abu da kaza da abu kaza yanzu baku yarda ba Mutane su tafi da Azuya da Rakumi, ku kuma ku tafi da Manzon Allah cikin tawagarku? Ba don Ladan Hijira ba da na zamanto daya daga cikin Mutanen Madina, kuma da ace Muta ne zasu bi wani kwari ko lungu, ni da nabi kwarinda Mutanen Madina suka haka ma lungun da suka bi don nuna don goyon bayansu, kuma Mutane zasu buya lallai cewa ku zaku gamu da tuntube bayana, to kuyi hakuri har ku gamu dani a tafkin Alkausara.

[Ingantacce ne] [Bukhari da Muslim suka Rawaito shi]

Yayin da Allah yai budi ga Manonsa na ganimomi masu yawa a yakin Hunain kuma bayan ya bar takunkumin da ya sanywa Ta'if kuma sai ya dawo mata da wasu ganimomi kuma maf yawan su Dabbobi ne kuma sun kai sama da Rakumi Dubu arba'in da da Dari da Ashirin na Dabbobisai Annabi ya bawa wasu Mutane sababbin shiga Musulunci don ya jawo hankalinsusai wasu daga cikin Mutanen Madina abun bai musu dadi ba amma manyan cikin su sun san ewa yadda Annabi yayi shi gaskiya yayin da Maganar su ta isar masa lokacin da wasu suka ce Annabi ya badaganima ga Mutanen da takubbunan mu suke digar jini daga yakarsu sannan ya kyale mu sai Annabi yayi umarnin da a tara su a wani wuri da ake kira kubba sai suka taru sai ya ce musu ya isarmun maganganun wasunku. har zuwa karshen abinda suka ce sai yai musu fada kuma sannan ya yi ikirari gare su abinda suka gabatar masa na taimako da kuma taimakonsu ga Musulunci da ya zo da shi sai ransu yayi dadi kuma suka san abu mai girma da Allah ya tanadar musu na zama da Annabinsa, da kuma dawowarsu tare da shi cikin tawagarsu, bugu da kari da abinda ya tanadar musu na ladan lahirasabida abinda suka gabatar na bajinta, sai Annabi ya Umarce suda hakuri akan abinda zai same su bayansa na juya musu baya. Taisir (306) tanbih Al'afham(3/403) Ta'asis Al'ahkam 93/197